Citation: Fallou Ngom (PI), Daivi Rodima-Taylor, Jennifer Yanco, Mustapha Hashim Kurfi, Garba Zakari, Babacar Dieng, and Rebecca Shereikis. 2022. "The Authentic Path." http://sites.bu.edu/nehajami/the-four-languages/hausa/hausa-manuscripts/hunwick-95-1-godaben-gaskiya/.

# Godaben Gaskiya

[Cover page]

Waƙar Nana Ɗiyar Shehu Usmanu

Tabbat Haqiqa da Godaben Gaskiya

da Tsorace-Tsoracen Tsayin Ƙiyama

da Sharaɗin Ƙiyama

Al-Nāshiru Ma'aikatar Tarihi

ta Sokoto Lambar Kati

P.M.B (Private Mail Box), 3180

Sokoto

[Page 2]

Bismi l-Lāh al-Raḥmāni al-Raḥīm. Ṣalla l-Lāhu ʿalā l-Nabiyyi

l-Karīmi. Shiʿru Asmāʾu, bint al-Shaykh al-Mujaddid,

Nūr al-Zamān, ʿUthmān ibn Fodio, taghammadahu Allāhu

bi raḥmatihi. Āmīn!

| | |
|---|---|
| Mu gode karimi Jallah Sarki mu sam huda | Da yayyimu ya 'aiko fiyayye Muḥammada |
| Da yazzaka yaffisshemu duffan ɓata duka | Da yabbamu Annuri da sunnar Muḥammada |
| Ka zaka da yai mana shi da addini mu zam yabo | Ga Allah Rahimi, wanda yasso Muḥammada |
| Da Ƙur'anu yazzaka yaffa duk bayyana mana | Hukunci da Sarki ya yi duk mubi Aḥmada |
| Da yabbayyana muna gaskiya duka mun jiya | Fasai kafiri fa da yaƙƙi hanyar Muḥammada |
| Ya Allah tsaremu shi ba mu shiriya mu sami bi | Ga hanyar shariʿah ko mu gana da Aḥmada |
| Salatu na Allahu shi dawama hakaza | Salamun gareshi yaffi kowa Muḥammada |
| Ka zaka da Allainai da sahbu da Tabiʿi | Da taɓi-taɓi duk ga turbar Muḥammada |
| Ku saurari waƙa ƴan uwa duka ku yi hattara | Ga hanya ku bar yin karkace ga Muḥammada |
| Mutu ba mu bar saɓo mu tsoraci Ubangiji | Mu kyauta ayukka ko mu sadu da Aḥmada |

[Page 3]

| | |
|---|---|
| Mu kyauta fa sallah wajibita garemu duk | Gama ita akkan duk ibada ga Aḥmada |
| Ku san fa idan ta kyautu addini shi kyautu | Duk garemu ga Allah ƴan uwa in ji Aḥmada |
| Gama ita zai Sarki ka dubi ga aikuna | Bawa da yazzam mumini ga Muḥammada |
| Mu zam ba da zakkah wajibita ga mai akwai | Da ḥajji ga mai iko da azumi musulmi Huda |
| Waɗanga fa su wa wajibi bisa mumini | Da yasshaida Allahu, yaffashedi Muḥammada |
| Ka zaka da alwala da wankan janabah duka | Da tsarkin kari duk wajibina ga Aḥmada |

Lalura idan ta kyautu to ayi taimama Fa don shi ashi Sunnah fa kena ga Aḥmada

Rashin fa ruwa, ciwo ka zaka da agaji Ga lato ƙasa ayi taimama inda Muḥammada

Ku zamka tsaron tsarkin tufa da jikinku duk Ku tsarkaka addini ku sadu da Ahamda

Ku zamfa biɗas sani ga addini, ku bar ɓata Ga hanya fa kar ku ɓace fa gobe ga Aḥmada

Gama da sani aka bin fa Allahu da Annabi Baṣira da sunnah dai ka kaimu ga Aḥmada

Ku zamka biɗar riba na guzuri ga Lahira Zamammu na duniya ko mu cimma Muḥammada

Ku san yin zikir da yawan karatu da nafilah Da azumi na lada su ka kammu ga Aḥmada

Ka zaka da wuridi da Addu'o'i da ƙoƙari Yawaita salati ga Annabinmu Muḥammada

Da ko hanƙurin wahalar ibadah da hanƙurin Talauci ka ba da fa ɗaukaka inda Aḥmada

Da ko hanƙuri bisa addara ta Ubangiji Da yaffa aza muna shi ka kaimu ga Aḥmada

[Page 4]

Da yardar hukunci duk na dazi da mai wuya Ka ƙara Musulmi duk daraja ga Aḥmada

Da sannan musulmi duk abinda fa kazzamo Kana so ka ganka fa kun ji halin Muḥammada

Da ko sadaqa daidai da iko ga dukiya Ka bada fa riba mai yawa ga Muḥammada

Fa in Alƙiyama ta zo yi niyya na firgita Da tsoro ga kowa sai fiyayye Muḥammada

Da babu uwa rannan da babu uba kurum Bale ƴan uwa mai agaji sai Muḥammada

Kwatamcin yininnan shekara fa dubu biyat Tsawo nai mu tsoraci Ubangiji mu bi Aḥmada

Mutane suna ce ba su motsi suna kurum Da tsoron fushin sarki da ya'aiki Aḥmada

Da baiyi fushi ba da ɗai kama tai da ba shi ko Fa gara fushi sarki da ya aiki Aḥmada

Waɗansu zufa ya kai ga baki shina gudu Fa tai musu lizzame na saɓon Muḥammada

Fa rana tana tafasa ga kanu da ƙolluwar Miyagu da sun kafa ƙaryata ga Muḥammada

Suna fa cikin wahala da yunwa da ƙishirwa Da ko zimuwar saɓo ga hanyar Muhmmada

| | |
|---|---|
| Wuta ko tana rura da tsawa a tsortata | Fa kowa shi firgita sai fiyayye Muḥammada |
| Mutane su bayyana duk da saɓonda sunka yi | Da babu wurin ɓoyo ga Allah na Aḥmada |
| Ku san masu cin riba cikkuna sun fi tuluna | Ga girma daɗa za'a a bayyana su ga Aḥmada |
| Su tashi kamar fa waɗanda Shaiɗan fa yattaɓa | Da Ƙur'anu yaffaza nasu hali ga Aḥmada |

[Page 5]

| | |
|---|---|
| Da mai zina ɗoi nai ya fi massai da ɗoi duka | Ana haɗa kora tai shi nisanci Aḥmada |
| Ku san annamimi hakaza da munafuki | Da mai sheda ƙarya ba su tsira ga Aḥmada |
| Harsunansu har ga gaba daɗa zasu fa bayyana | Zama ba su samunsu fa ceto ga Aḥmada |
| Da masu fa girman kai ga duniya da zulmu duk | Haƙiƙa wazanga fa ba su gamo da Aḥmada |
| Da mai riya ko da yai ibadah tsubi-tsubi | Suna tashi ba shi isa da su ga Aḥmada |
| Da mai cin gululu da rashwa, mai cin haramu duk | Ku san ba su samun ceto ga Aḥmada |
| Da mai kisa ko hakana da algussu don su san | Fa ba su cikin jama'a ta Annabi Aḥmada |
| Da mai rena ko maganar uwaye da mai raɗa | Da mai hassada duk ba su tsira ga Aḥmada |
| Wuta fa kasatar masu sata ana tsaye | Kaza fa da mai ƙwace tagotai ga Ahmada |
| A gargaɗi: kafirrai zuwa wuta nan-da-nan | Gabanin hisabi masu ƙi nasa Aḥmada |
| Tsayin fa daɗa in ya yi tsanani da firgita | Musulmi fa suna kiran fiyayye Muḥammada |
| Su zo su ga Adamu har su zo su ga Nuhu duk | Su ce musu yau sai Annabiyu Muḥammada |
| Su ce yau ku zo ga Khalilu Sarkinmu yai fushi | Khalilu shine yau sai fiyayye Muḥammada |
| Ku zo ku ga Musa shi da ʿIsah su zo duka | Su ce babu dama yau fa sai ko Muḥammada |
| Su zo ga fiyayyen talikai duka shi shi ce | Fa ni ɗai ka ceto yau ga Allahu Aḥmada |

[Page 6]

| | |
|---|---|
| Shi zo fa da sarki yai fushi shi da ya'isa | Shi girmama sarki shiyi sujada Muḥammada |

| | |
|---|---|
| Shi ce masa roƙi abaka komai da kabbiɗa | Ana bakashi ya kai masoyi Muḥammada |
| Shi ce masa Rabbi ummati ummati duka | Karimi shi ce na ba ka ceto Muḥammada |
| Shi kami abada awon ayyuka shina tsaye | Waɗansu ga tsira sai da ceto ga Aḥmada |
| Waɗanda suna awon ayyukansu sunka je | Ga rannan kathīran suna tare da Aḥmada |
| Waɗanda miyagun ayyukansu sunka fi | Ga rannan ka hallaka sai da ceto ga Aḥmada |
| Abada takardu waɗansu dama waɗansu ko | Ga hauni waɗannan sun yi nisa ga Aḥmada |
| Aba masu alhurma fa ceto da sunka bi | Ga hanya ta sunna sunka bi da Aḥmada |
| Da ko annabawa haka za salihīna duk | Waliyyai kaza masana da sunka bi Aḥmada |
| Daɗa a naɗe ƙasa a kawo siraɗi kau | Tsakanin wuta aka fa mu haushi da Aḥmada |
| Ku san ya fi gashin kai ƙaramci fa ya fi ko | Ta kobi ga kaifi mun jiya ga Muḥammada |
| Shina fa da tozo har bakwai wallah anka ce | Na farin waɗansu ka rarraba da Muḥammada |
| Idan babu iman shiya fa ba a wuce ga nan. | Mu fuskanci Allah ƴan uwa da Muḥammada |
| Gama ba wurin bi sai siraɗi a tsira duk | Bisa ƙaddara sarki da yaffaɗa Aḥmada |
| Ga tozo na biyu sallah fa nan anka tambaya | Na ukku fa zakkah, kai mu zan bin Muḥammada |
| Ga tozon huɗu azumi fa haji na kau biyat | Na shidda fa alwala ta hiyyar Muḥammada |
| Ga tozon bakwai aka tambayar Nana alhakin | Uwaye mutu ba mu tsira tare da Aḥmada |

[Page 7]

| | |
|---|---|
| Waɗansu su shuɗe nan-da-nan ba wuya kurum | Kamar walƙiyar hadari fa tare da Aḥmada |
| Waɗansu kamar bisa ingarmu waɗansu ko | Ga zafi awa iska su zo da Muḥammada |
| Waɗansu awa tafiya ƙafafunsu dai suke | Bisa ga siraɗi har su zo ga Muḥammada |
| Waɗansu fa jan ciki sukai wasu rarrafe | Fa mai jan ciki fa ka faɗo in ji Aḥmada |
| Ga tozon bakwai na siraɗi nan a munafake | Shike faɗowa wuta kai mu gaskanta Aḥmada |

A ruɗai kamar ruɗinda yai wa Ubangiji | Fa duniya da addini da shi da Muḥammada

Waɗanda ayyuka sunka daidaita anka ce | Fa su anka kai la'rafu in ji Muḥammada

Ajiddah daɗa Alkausara don a sha ruwa | Fa tafkin fiyayye annabinmu Muḥammada

Fa nan aka korar mai musa ya ga sunnata | Ba ya sha ruwan Alkausara inda Aḥmada

Da mai badawa waɗanda duk anka tambaya | Isa inda manya masu tambayar Muḥammada

Fa sun fi zuma daɗi da madara fa sun fi | Ko turare na miski fa mun jiya ga Muḥammada

Ruwannan farinsa fa ya fi madara fa wa'iya | Misalin kwatancin Kausara sai Muḥammada

Akwai lidduwa wa na lu'u-lu'u ko na sha nasa | Kwatamcinsu dai fa da annabawa ga ko ƙida

Kwatancina faɗi nai fa tafiyar wata shike | Fa kussha ruwan Alkausara shiga Aḥmada

Fa nan aka barka duda guda ana rawa | Da murna na tsira an ga hasken Muḥammada

Zuma za a kwankwaɗa sai a ɗunguma jannata | Fa darussalami garin masoyan Muḥammada

[Page 8]

Fa kussha su bashi fa ƙari ƙishirwa daɗa | Zama ya sani ya tsira da Aḥmada

Fa Allah shi bamu mu shasu rannan mu tsira duk | Da girman fiyayye annabinmu Muḥammada

Mu tuba, mu kyauta ƴan uwa ko mu san fita | Waɗanga haɗurra don fiyayye Muḥammada

Mu ya da ta duniya ba gida ce ba sai kufai | Mu zaɓi gidan Aljannah shi aggidan wadata

Mu zanna mu sha daɗi da madara, mu sha zuma | Muna fa cikin ni'imammu tare da Aḥmada

Da babu mutuwa tutub muna zamne sarmadan | Tutub kowa cikin shawa da sarawa duka

Tutub kowa cikin shawa da sarawa duka | Muna yi cikin Aljannah mun ga Muḥammada

Cikin inuwa ko ga abinci iri-iri | Da ba a kwatance nai kurum inda Aḥmada

Gidajenmu zinarru, tufafi na al-harīr | Mu sha Salsabīlu da Zanjabilu ga Aḥmada

Jikinsa kamar Yaƙūtu Marjanu ai da ko | Ƙawassu da jawhar tadashi da Zabarjada

Citation: Fallou Ngom (PI), Daivi Rodima-Taylor, Jennifer Yanco, Mustapha Hashim Kurfi, Garba Zakari, Babacar Dieng, and Rebecca Shereikis. 2022. "The Authentic Path." http://sites.bu.edu/nehajami/the-four-languages/hausa/hausa-manuscripts/hunwick-95-1-godaben-gaskiya/.

Da ba su fa ɓacin zuciya ba su tuntuni
Tutut sai karama sai fa duba da Aḥmada

Fa na su suke daidai da Ḥūru ga shekara
Tutut sai karama suna duba da Aḥmada

Katangar azurfa ga shigiffu na lu'u-lu'u
Waɗansu nako zinariya in ji Aḥmada

Ku santa ƙasar Aljannah Tibru da zafaran
Fa ƙamshinta ya fi na miski in ji Muḥammada

Akwai wani daɗi wanda yaffi na jannata
Ganin jAllah Sarki, wanda yazzaɓi Aḥmada

Idan mun ga Allah sannu sai mu mance da jannata
Da daɗi na dubin wanda ya 'aiki Aḥmada

Zama can jama'a duk fa wasa suke zuwa
Ganinai Taʿāla wanda yayyi Muḥammada

[Page 9]

Akwai wasu tsuntsaye da muryarsu taffinan
Ga goge da daɗi duk su ji su da Aḥmada

Waɗanda ka saurara ma goge na duniya
Ba su samun saurarensa can da Aḥmada

Fa Allah shi ba ganin fiyayyenmu mu duka
Zamu shi kakimu ga jAllah mai son Muḥammada

Fa Allah cika muna wanga guri da munka yi
Fa don martaba tai annabinmu Muḥammada

Shi ban gafarar thanbin da niyyi shi bani kau
Shiga wagga niʿmah don fiyayye Muḥammada

Fa domin darajjar Shehu jaili da Ahmadu
Arrufaʿ da badwi har da Sūfi na Aḥmada

Fa domin darajjar Al-Shaykhu Uthmanu Fodiyo
Da yassami tsani nan gareshi da Aḥmada

Da Alhurmacinsu a ba mu nasara ya Ubangiji
Da girman fiyayye annabinmu Muḥammada

Ashafe siraɗi katha shibru da anka duk
A ɗauka addini da girman Muḥammada

A shafe fa ka firci gabas du da yamma duk
Da dama da haunin Ubangiji don Muḥammada

A kawo atiƙu gidan nasara da ɗaukaka
Garemu taʿala, wanda yayyi Muḥammada

Da jama'ar Musulmi duk da sutura da lafiya
Fa domin darajja tai fiyayye Muḥammada

Fa kowabbiɗa ga Muhammadu shi ba ya rasa
Ga Allah haƙiƙan ya fi kowa Muḥammada

Ku san zuciyata ta yi hasken farin ciki — Da murnar kiran sunan fiyayye Muḥammada

Zama guzurina ni fa ke nan ga duniya — Garai nika tamma tai da ceto ga Aḥmada

Daɗa kun ji waƙa ƴan uwa nan fa taccika — Fa Allah shi karɓa don fiyayye Muḥammada

[Page 10]

Shi gafarta inna ta da baba da ƴan uwa — Musulmi shi bamu ganin fiyayye Muḥammada

Ka zaka thuriyya har abokin zama duka — Masoya fa domin annabinmu Muḥammada

Fa ku tambaya kowayyi waƙar ga duk ka ce — Da shi Nana ta ƴar Shehu mai son Muḥammada

Ku dai muna niyya ƴan uwa don ku bi ta duk — Ku samu ku daidaita ga hanyar Muḥammada

Zama mumini in ya ji waʿzu shi san — Daɗi na riba da amfani ga sunnar Muḥammada

Fa na gode Allah nai salatai da sallama — Bisa ga fiyayye Al-Rasūlu Muḥammada

Kadhāka da Allai nai da ṣahbu da tabiʿ ī — Da tabi-tabi ina duk ga turbar Muḥammada

Cikin shekara ta Bina'u Rushdin gali sabiʿī — Na Ramzi afa hijrah tai fiyayye Muḥammada

Ƙidan kuwa shekara duk na waƙar don ku san — Ɗari da talatin na da biyu ku bi Aḥmada

Tammat bi hamdi l-Lāhi wa ḥusni ʿawnihī

Wa ṣalātu wa salām ʿalā

Sayyidinā Muḥammad

ṣalla l-Lāhu ʿalayhi

wa sallam